Tarihin Ahlul Baiti (A.S)
Daga Cibiyar Ahlul Baiti Da Sahabbai ta Najeriya

كتاب نجي كربلاء للشيخ عبد العزيز العمير بلغة الهوسا

ترجمه محمد المنصور إبراهيم

# Mai Rabon Ganin Baxi

## Tarihin Zainul Abidina Ali Xan Husaini Xan Ali Xan Abu Xalib (A.S)


Wallafar
Sheikh Abdul Aziz binu Ahmad Al Umair
Alqali a kotun qoli ta shari'ar musulunci
a qaxif ta qasar Saudia

Fassarar
Muhammad Mansur Ibrahim
Cibiyar Nazarin Addinin Musulunci
Ta Jami'ar Usmanu Xan Fodiyo, Sakkwato

Waxanda suka buga
Mu'assasatu Ahlil Baiti Wassahabah, Najeriya

Bugun Farko 1427H/2006M
Adadin da aka buga: Kwafi 75,000
ISBN 978-2076-68-5

© Haqqen buga wannan littafi na Mu'assasatu Ahlil Baiti Wassahabah, Najeriya ne.
Wanda yake son buga shi saboda Allah ya na iya tuntuvarmu a adireshinmu kamar haka:
97, Ahmadu Bello Way, P.O.Box 2491,
Sokoto, Najeriya.

Ko kuma ya tuntuvi Mai Fassara a
mansursokoto@yahoo.co.uk

# ABUBUWAN DA KE CIKI

Gabatarwa...............................................
Muhimmancin Sanin Tarihi:..................
Qa'idodin karanta tarihi:.......................
Qa'ida ta Xaya: Mai karatu ya qudurta koyi da magabata:..................................................
Qa'ida ta Biyu: A kula da ingancin labari ko rashin ingancinsa:........................................
Qa'ida ta Uku: Sanin cewa, mutum duk xan tara ne:...............................................................
Qa'ida ta Huxu: A tsarkake zuciya:.............
Qa'ida ta Biyar: A mutunta Malamai da ladabi wajen ambatonsu.........................................
Qa'ida ta Shida: Hattara da sukar Malammai:
Qa'ida ta Bakwai: Adalci shi ne, auna yawan sawabar mutum tare da yawan kurakuransa.....
Taqaitaccen bayani akan matsayin gidan annabta................................................
Yadda mutane su ka kasu kashi uku a game da *Ahlulbaiti*......................................................
Kashi na farko: Su ne waxanda su ke tauye haqqensu.........................................................
Kashi na biyu: Su ne waxanda su ka faifaye a wajen sonsu......................................................
Kashi na Uku: Su ne waxanda su ka tsakaita, su ka tsaya kan gaskiya.........................................
FASALI NA XAYA:
Wane ne Zainul Abidin?...........................
Sunansa da Haifuwarsa.............................
FASALI NA BIYU:
Jihadinsa Da Yadda Ya Kuvuta A Karbala'.................................................
FASALI NA UKU:
Yabon da Mutane su kayi ma sa.................
FASALI NA HUXU:
Yawan Ibadarsa da qanqan da kansa ga Ubangiji.................................................
Sallarsa da yawan addu'arsa.......................
Yadda ya ke tsoron Allah da dogaro ga reshi.......................................................
Karimcinsa da yawan sadaqarsa.....................
FASALI NA BIYAR:
Yawan Ilminsa.................................................

FASALI NA SHIDA:
Kulawarsa da tsarkake zuciya......................
Tawali'unsa:...........................................
Haqurinsa:..............................................
Afuwa da Rangwame:................................
Yarda da qaddarar Allah:............................
Tsentseni:..................................................
FASALI NA BAKWAI:
Wannan Ita ce Aqidarsu............................
Na xaya: Su na sallah bayan ko wane musulmi.................................................
Na biyu: Sun yarda da Sahabbai.................
FASALI NA TAKWAS:
Wafatinsa................................................
Kammalawa
Darussa daga abin da ya gabata:
Darasi Na xaya: Tataccen tauhidi shi ne aqidar da *Ahlulbaiti* su ka rayu akansa...........................
Darasi Na biyu: Kyakkyawar alaqar da ke tsakanin Sahabbai da *Ahlulbaiti*, iyalan gidan Manzon Allah (SAW)........................................
Darasi na Uku: Irin kyawawan xabi'un wannan bawan Allah......................................................
Darasi na Huxu: Cikakken tsoron Allah shi ne wanda ya ya ke gadar da yin aiki da tsare ibada...................................................................
Darasi na biyar: Qarya ne ace Ahlus Sunnah su na gaba da *Ahlulbaiti* a da ko a yanzu.................................................................
Daga qarshe....................................................

## Bismillahir Rahmanir Rahim

## Gabatarwa

Godiya ta tabbata ga Allah wanda ya bude qofofin imani don masu shiga, ya sauqaqe hanyoyin kyautatawa ga masu nema, ya shimfixa rahamarsa ga masu ibada, ya saki labulen suturarsa don gafartawa masu tuba.

Na shaida babu wanda ya cancanci bauta sai Allah, Shi kaxai. Na shaida cewa, shugabanmu Muhammadu bawansa ne, Manzonsa, wanda aka aiko shi da littafi mafi kyawo, aka qarfafa shi da kyawon bayani da rarrabe zance. Allah ya yi tsira gare shi da dukkan iyalansa da Sahabbai, salati da tsira madawwama zuwa ranar haxuwa da hisabi.

Bayan haka, Lallai sanin matsayin Manzon Allah (SAW) matsayi ne shi kansa babba. Harshe ba zai gaji ba da bayanin darajojinsa ballantana alqalami. Sonsa sharaxi ne na Imani, darajanta shi kuwa shi ne

alamar tsoron Allah. Imani bai kammala sai harshe ya furta qaunarsa, zuciya ta qullu akan sonsa da jivintarsa, da darajanta shi da biyar hanyarsa. Ya na daga cikin sharuxxan son Manzon Allah (SAW) a so iyalansa tsarkakakku domin alaqarsu da wannan asali mai daraja na shugaban Manzanni, jagoran masu tsoron Allah.

Son Manzon Allah (SAW) ga 'yarsa Fatimah tabbatacciyar magana ce da dukkan masana sun san da ita, haka kuma 'ya'yanta Al Hassan da Al Hussain waxanda su ne farin cikin Manzon Allah (SAW) da hasken zuciyarsa a duniya. Don haka ne na ga dacewar in ba da kyakkyawan misali daga tsarkakakkar zuri'arta, in rubuta tarihin jikanta na wajen xanta Hussaini kuvutaccen karbala (AS) domin mu samu wani haske daga tarihinsa musamman a wannan zamani da gaskiya ta cakuxa da qarya, mavarnata kuma sun rataya da gaskiya don rufe varnarsu, su na yaudara da sunan son iyalan Manzo (SAW).[1]

Da sannu mai karatu zai gano irin darajojin wannan taliki, tsarkakakkiyar nasabarsa, zurfin hankalinsa, nisan tunaninsa, tarin ilminsa, kyawon ibadarsa da kuma tsarkin zuciyarsa ba tare da wani qarin gishiri ko zuqi ta mallau ba.

Na yi shimfixa gabanin wannan taqaitaccen tarihi da wasu dokoki da ya wajaba ga mai karatun tarihi ya kiyaye su, na biyo su da wani gajeren bayani akan son iyalan gidan Manzo (SAW) saboda muhimmancinsa. A cikin tarihin wannan bawan Allah kuwa na dogara ga ingantattun ruwayoyi daga littafan magabata, na kuma taqaita sharhi akansu domin sauqin fahimtarsu ga mai karatu. A qarshen littafin na bayyana sakamakon wannan nazari. Idan na yi daidai baiwa ce daga Allah. Idan kuma kuskure ya shiga cikin aikina to, daga wurina ne da wurin shaixan. Fatar da ni ke Allah ya haxa ni da sawaba, kuma ya yafe kurakuraina.

Ya Allah! Ina shedar ma ka qaunata ga iyalan Manzonka, irin qaunar da ni ke fatar samun cetonsa akanta, da kusanci zuwa ga reka a dalilinta. Ya Allah! Ka haxa ni da masoyan nan nawa Muhammad da tsarkakan iyalansa da nagartattun sahabbansa da masu bin sawunsu har zuwa ranar alqiyama a cikin aljannarka maxaukakiya.

---

[1] Masana sun qari juna sani game da *Ahlulbaiti* iyalan gidan Manzon Allah (SAW). Magana mafi rinjaye ita ce cewa, *Ahlulbaiti* su ne waxanda aka haramta masu cin sadaqa daga Banu Hashim da Banul Muxxalib saboda dangantakarsu da Manzon Allah (SAW). Duba: *Nailul Auxar,* na Imam As Shaukani, a Babin dalilin fassara iyalan Manzon Allah waxanda ake sanyawa ga salati (2/77), da kuma *Jala'ul Afham,* na Shehun Malami Ibnul Qayyim, Shafi na 109.

# Muhimmancin Sanin Tarihi:

Ya na da kyau mu soma magana anan da nazarin faxar Allah Ta'ala in da ya ke cewa,

﴿أُولَئِكَ الَّذِينَ هَدَى اللَّهُ فَبِهُدَاهُمُ اقْتَدِهِ﴾

Ma'ana:

"Waxancan su ne waxanda Allah ya shiryar, to, ka yi koyi da shiriyarsu". An'am 90

Wannan aya ta kan sa ka tuna sunayen manya waxanda ayyukansu su ka dawwamar da ambatonsu, gurabunsu su ka fito da sunayensu, tun daga tarihin Annabawa, waxanda su ka haskaka duniya da hasken shiriyarsu har ya zuwa tarihin Sahabbai waxanda tarihinsu ya ke walqiya a cikin sauran tarihin 'yan adam[2], har zuwa ga tarihin malamai da sauran mutanen kirki, shugabanni da talakkawa[3]. A cikin tarihinsu za ka ga mutanen da su ka sadaukar da rayuwarsu wajen bayanin gaskiya da hukunci da shari'a da yaxa addini, ga kuma yawan ibada da istiqama, abin da zai sa ka yi murna da alfaharin zamanka cikin wannan al'umma wadda ta saba fitar da jarumai masu jagorancin duniya. Anan ne za ka daxa gane haxarin jahiltar da mu ka yi da ilmin tarihi da hasarar da ta cim mana a sakamakon haka.

Karanta tarihin wani bawan Allah ya kan ba ka damar sanin halayyarsa da ilminsa da sauye sauyen da ya samu a matakan rayuwarsa. Daga nan ne za ka xauki darussan da za su taimaka wajen gyara rayuwarka da kauce ma miyagun ayukka waxanda zasu qazamta al'amarinka, ta haka sai a samu musulmi na gari waxanda ke iya xaukar nauyin ci gabantar da al'umma a gaba.

Ga wasu daga cikin maganganun magabata waxanda ke nuna muhimmancin ilmin tarihi:

Imam Abu Hanifa (RH) yace, Na fi sha'awar karanta labarin malamai da kyawawan xabi'unsu fiye da karanta ilmin fiqhu domin wannan shi ke karantar da ladubbansu da halayensu.[4]

Imam Al Sakhawi yace, Rayuwar na gaba ita ce madubin na baya.

Imam Muhammad binu Yusuf yace, Ban tava ganin abin da ya ke da amfani ba kamar karanta labarin mutanen kirki.[5]

---

[2] Za ka iya samun cikakken tarihin Sahabbai a waxannan littafai; *Al Isabah fi tamyizis Sahabah*, na Ibnu Hajar Al Asqalani, da *Usdul Gabah fi Ma'rifatis Sahabah,* na Ibnul Asir, da kuma *Al Isti'ab fi Ma'rifatil Ashab,* na Ibnu Abdil Barri Al Qurxubi.

[3] Waxannan kuma tarihinsu ya na a cikin *Siyar A'lam An Nubala'* na Imam Dhahabi, da *Hilyatul Auliya',* na Abu Nu'aim, da *Al Xabaqat Al Kubra,* na Ibnu Sa'ad da sauransu.

[4] Duba gabatarwar da aka yi a bugu na biyu na littafin *Risalatul Mustarshidin,* na Haris Al Muhasibi, tahaqiqin Ustaz Abdul Fattah Abu Guddah, Shafi na 12.

Babban masani Ibnul Jawzi yace, Ina ba ku shawarar karanta tarihin magabatan kirki da littafansu da labaransu. Wannan zai sa ku zama kamar ku na ganinsu.Kamar yadda wani mai hikima yace,

Na kasa samun ganin gidajensu da idanuna, amma zai yiwu in ga gidajensu da kunnuwana.

Wani kuma yace,

Sun kasance su ne qawar duniya a lokacin rayuwarsu,
Kuma su a bayan mutuwarsu su ke qawata tarihi da littafai.[6]

Don haka, ya kai xan uwana mai karatu! Kutsa kanka sosai a cikin fadamar tarihi don ka sha ni'ima a cikin inuwar bishiyoyinta, ka ni'imtu da kallon daxaxan furanninta da xanxanar zazzaqan ababen shanta.

---

[5] Duba littafin da ya gabata, kuma a wannan shafin.

[6] Wani baitin waqe ne da yazo a cikin littafin *Saidul Khaxir,* na Ibnul Jauzi, Shafi na 448.

# Qa'idodin karanta tarihi:

Qa'ida ta Xaya: Mai karatu ya qudurta koyi da magabata:

A yau mu na fama da qarancin aiki tare da tarin ilmi. Duba yawan ayoyin da mu ka sani da hadissai da labaran magabatan kirki waxanda ya kamata ace mu na aiki da su kamar yadda Allah yace:

﴿أُولَئِكَ الَّذِينَ هَدَى اللَّهُ فَبِهُدَاهُمُ اقْتَدِهِ﴾ الأنعام ٩٠

Ma'ana:

Waxancan su ne waxanda Allah ya shiryar, To, kayi koyi da shiriyarsu.

Ga wani misali mai muhimmanci game da koyi da Manzon Allah (SAW) a wurin magabata. Bukhari ya fitar da hadisi a cikin ingantaccen littafinsa[7] cewa, Abdullahi xan Umar (RA) ya kasance ya na kiyaye wuraren ibadar Manzon Allah (SAW) a hanyoyin Madina, sai a gan shi ya na sallah a wasu wurare waxanda Manzon Allah (SAW) ya yi sallah a cikinsu. Har ma da akwai wata bishiya wadda Manzon Allah (SAW) ya yi sallah a qarqashinta Ibnu Umar ya rinqa kula da ita ya na ba ta ruwa don kada ta mutu.[8]

Shugaban mabiya Sunnah Ahmad binu Hambali yace, ban tava rubuta wani hadisi ba sai na yi aiki da shi. Watarana sai na cimma hadisin da yace Annabi (SAW) ya yi qaho, ya bai wa wanzamin Abu Xaibah dinari xaya, sai na yi qaho na bai wa wanzami dinari xaya don in yi koyi da shi.[9]

Ibrahim binu Hani yace, Ahmad xan Hambali ya nemi in samar ma sa wani wuri da zai vuya har kwana uku, sai nace ma sa, ya na da wahala ga reka baban Abdullahi. Sai yace, ba kome, idan ka yi zan saka ma ka. Da na samar ma sa wurin ya qare kwana uku ya fito sai yace min, Manzon Allah (SAW) ya vuya a cikin kogo lokacin da ya yi hijira. Bai kamata mu yi koyi da shi a wurin daxi mu daina koyi da shi a yanayin wahala ba.[10]

Kamar haka ne mu ke da buqatar gina al'umma wadda ke matuqar kula da aiki irin kulawarta da sanin abin da ta jahilta. Da haka ne mu ke iya samun albarkar karatu, mu ke bin hanyar waxanda Allah ya yi ni'ima akansu, ba waxanda Allah ya yi fushi da su ba, ba kuma vatattu ba.

---

[7] Duba *Sahihul Bukhari,* a Kitabus Salati, Babin masallatan da ke akan hanyoyin MAdina, Hadisi na 461.

[8] A nan ya na da kyau mu lura cewa, Ibnu Umar ya na neman albarkacin aiki ne ba albarkacin wuri ba. Koyi da Manzon Allah (SAW) anan shi ne manufa ba wuraren ba. Duba labarin a cikin *Siyar A'lam An Nubala'* (3/213).

[9] Duba littafin *Al Manhaj Al Ahmad fi tarajumi Ashabi Ahmad* (1/93).

[10] Duba littafin da ya gabata.

**Qa'ida ta Biyu:** A kula da ingancin labari ko rashin ingancinsa:

Da daxewa maqiya su ka kewaye musulmi. Sun shigar da hadissan qarya da labarai marasa tushe a cikin tarihinmu. Sun gurvata wasu daga littafan tarihi da irin miyagun aqidunsu, sun kuma haddasa fitinu a tsakaninmu. Sun sanya savani da rashin jituwa sun yawaita a tsakanin musulmi. Amma duk wannan bai hana malaman musulunci su yi aikin da Allah ya xora ma su ba na tantance gaskiya da qarya. Sun yi wannan ne kuwa ta hanyar bibiyar asalin ko wace magana da in da aka samo ta. Wannan shi ake kira ilmin isnadi.

Imam Ibnul Mubarak yace, Isnadi ya na daga cikin addini. Ba don isnadi ba kuwa da kowa ya faxi abin da ya ke so.[11]

Shu'ubah yace, Duk hadisin da ba ya da "Haddasana" a cikinsa zulala ne kawai tun da ba a san asalinsa ba.[12]

Shugabannin *Ahlulbaiti* da daxewa su ka koka game da yawaita qarya da masu da'awar sonsu suke ma su. Ja'afar Al Sadiq yace, Mu *Ahlulbaiti* mutane ne masu gaskiya. Amma ba mu rasa maqaryaci da ke zuqa mana qarya don ya shafa mana kashin shanu a idon mutane.[13]

Don haka ya zama dole mu kula da wannan ilmin na isnadi da Allah ya kevanci wannan al'umma da shi, wanda kuma ya ke buqatar mu san maruwaita mu kuma yi amfani da kaifin basira wajen tantance kalamansu da rarrabe gaskiya daga qarya kamar yadda maqera su ke rarrabewa tsakanin zinariya da sanholama.

**Qa'ida ta Uku:** Sanin cewa, mutum duk xan tara ne:

Rauni da Jahilci da Kuskure da Mantuwa kaxan ne daga cikin halayen xan adam da Allah ya halicce shi da su. Manyan shugabanni da zavavvu mutanen kirki duk su na cikin faxar Allah Ta'ala da yace,

﴿وَخُلِقَ الْإِنْسَانُ ضَعِيفًا﴾ سورة النساء: ٢٨

**Ma'ana:**

Kuma an halicci xan adam mai rauni.

Haka kuma su na cikin faxar Manzon Allah (SAW) da yace, "Ko wane xan adam mai yin kuskure ne. Kuma mafifitan masu kuskure su ne masu tuba".[14]

---

[11] Duba gabatarwar *Sahihu Muslim,* Shafi na 78.

[12] *Al Muhaddisul Fasil*, Shafi na 6

[13] *Ikhtiyaru Ma'rifatir Rijal,* na Xusi (1/324) da *Biharul Anwar,* (2/217) da *Mustadrak Al Wasa'il,* na Xabarsi (9/90).

[14] Tirmidhi ne ya fitar da shi a littafinsa, daga hadisin Anas, Hadisi na 2423, a cikin Kitabu Sifatil Qiyama, da kuma Ibnu Majah a nasa littafin, Hadisi na 4241, a littafin Zuhdu, Babin tuba.

Wannan magana ba ta faku ba daga zukatan bayin Allah mutanen kirki don kuwa sun yawaita faxarta a tsakanin masoyansu da mabiyansu. Misali, Imam Ja'afar binu Muhammad Al Sadiq (AS) yace, Ina sheda ma ku cewa, ni jikan Manzon Allah ne (SAW) amma ba ni da wani tabbacin kuvuta daga wuta sai ga aikina. Idan na bi Allah zai rahamshe ni, idan kuwa na sava ma sa zai yi mana azaba mai tsanani.[15]

Imam Malik binu Anas shi ma ya na cewa, Ni mutum ne da ke iya yin kuskure kamar yadda ni ke iya yin daidai. Don haka ku duba fatawata duk in da ta dace da Alqur'ani da Sunnah ku yi riqo da ita, in da kuwa ta sava ma su ku bar ta.[16]

Daga nan zamu fahimci cewa, masu cewa Imamai da Waliyyai ma'asumai ne su na zurfafawa ne kawai a cikin sha'aninsu, su na fitar da su daga 'yan adamtakarsu. Wannan ya fi zama suka a ga resu fiye da yadda ya ke yabo akansu.

**Qa'ida ta Huxu:** A tsarkake zuciya:

Tsarkin niyya sifa ce ta masu gaskiya. Mutum nawa ne ke maganar adalci amma a aikace za ka ganshi mai biye ma son zuciya, mai kau da kai daga hujjojin Shari'a, Sai ya hukuntar da hankalinsa ya vace ya vatar da mutane? Allah Ta'ala ya yi gaskiya da ya ke cewa,

﴿وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّنَ اتَّبَعَ هَوَاهُ بِغَيْرِ هُدًى مِنَ اللَّهِ إِنَّ اللَّهَ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الظَّالِمِينَ﴾ القصص: ٥٠

**Ma'ana:**

Wane ne ya kai yawan vata daga wanda ya bi son ransa ba tare da shiriya daga Allah ba? Lalle ne Allah ba ya shiryar da mutane azzalumai.

Me ya raba irin waxannan da mutanen jahiliyyah waxanda aka san su da hankali da basira amma da manzo ya zo ma su da abin da ya sava ma aikin iyayensu sai su ka buga kai a qasa su ka qi yarda su na masu cewa,

﴿إِنَّا وَجَدْنَا آَبَاءَنَا عَلَى أُمَّةٍ وَإِنَّا عَلَى آَثَارِهِمْ مُقْتَدُونَ﴾ الزخرف ٢٣

**Ma'ana:**

Mu, mun sami ubannenmu a kan wata hanya, kuma lalle ne mu muna tafiya akan sawunsu.

To, ina basirarsu ta ke? Ina gwanintarsu ta je ne?

Mu na buqatar mu tsaya mu lurar da kawunanmu cewa, gaskiya ita ce ta fi cancanta a bi ta akan kome. Kuma duk abinda ya sava ma gaskiya, magana ce ko aiki, aqida ce ko ra'ayi, mu yi watsi da shi. wanda ya zo

[15] *Aqidatu Ahlilbaiti,* na Abdullahi Al Khudair, Shafi na 27, daga *Rijal Al Kasshi,* Shafi na 225-226.

[16] *Jami' Bayan Al Ilim Wa Fadlihi,* (2/32).

mana da gaskiya mu karva, wanda ya zo da savaninta mu bar shi da kayansa ko wane ne shi, tare da qaunarsa da girmama shi idan ya cancanci a qaunace shi ko a girmama shi. Mu tuna irin tambayar da za a yi mu na a gaban Allah ranar alqiyama, ita ce;

﴿مَاذَا أَجَبْتُمُ الْمُرْسَلِينَ﴾ القصص (٦٥

Ma'ana:
Da me kuka karva kiran manzannina?

Qa'ida ta Biyar: A mutunta Malamai da ladabi wajen ambatonsu

An karvo daga Ubadah binu Samit yace, Manzon Allah (SAW) yace, Duk wanda bai mutunta manyanmu, bai tausaya ma qanananmu, kuma bai san haqqen malamanmu ba, to, wannan ba shi a cikin al'ummata.[17]

Malam Xawus binu Kaisan yace, Yana daga cikin sunnah a darajanta mutane huxu: Malami, da Tsoho mai furfura, da Sarki, da Mahaifi.[18]

Don haka, wajibin musulmi ne ya darajanta Malami, ya mutunta shi, ya yi ladabi a wajen faxin sunansa tare da yi ma sa addu'ar samun rahama da gafara, ko malamin ya na raye ne ko bayan mutuwarsa. To, musamman kuma idan malamin ya kasance fitacce ne wajen taimakon gaskiya da yaxa sunnah da tozarta qarya da tarwatsa mutanenta.

Malam Abu Zur'ah Ar Razi yace, Ina tare da Ahmad xan Hambali sai aka ambaci Ibrahim binu Xuhman, xaya daga cikin malamai na Allah, a lokacin Ahmad ba shi da lafiya ya na kwance amma nan take sai ya tashi zaune, yace, bai kamata a ambaci mutanen kirki ba muna kwance.[19]

Qa'ida ta Shida: Hattara da sukar Malammai:

Musulunci ya haramta musulmi ya soki xan uwansa musulmi ko wane iri ne. Maimakon haka an umurce mu da mu kyautata magana ga junanmu da abin da zai faranta rayukanmu. Wannan wajabcin ya na daxa qarfafa ga haqqen malammai na Allah waxanda ke isar da addininsa su na karantar da mutane yadda za su bi gaskiya.

Kasa kunnenka ka ji wani labari da zai tabbatar maka gaskiyar abinda na ke faxa;

Wasu mutane daga cikin munafikai sunyi izgili da wasu alarammomi daga cikin sahabbai su kace, ba mu tava ganin makwaxaita

---

[17] Imam Ahmad ne ya ruwaito shi daga Hadisin Ubadah binu Samit, Hadisi na 21693 a cikin Musnadul Ansar.
[18] Al Bagwi ya kawo shi a *Sharhus Sunnah,* (13/43).
[19] *Tahzib Al Tahzib,* (1/148).

masu qarya da tsoro kamar makarantan nan namu ba.[20] Sai Allah ya saukar da Alqur'ani ya na tona asirinsu da ire irensu in da ya ke cewa,

﴿وَلَئِنْ سَأَلْتَهُمْ لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلْعَبُ قُلْ أَبِاللَّهِ وَآيَاتِهِ وَرَسُولِهِ كُنْتُمْ تَسْتَهْزِئُونَ (٦٥) لَا تَعْتَذِرُوا قَدْ كَفَرْتُمْ بَعْدَ إِيمَانِكُمْ إِنْ نَعْفُ عَنْ طَائِفَةٍ مِنْكُمْ نُعَذِّبْ طَائِفَةً بِأَنَّهُمْ كَانُوا مُجْرِمِينَ (٦٦)﴾ سورة التوبة

Ma'ana:
Kuma lalle ne idan ka tambaye su zasu ce, mu dai kawai mun kasance muna kutsawa ne muna wasa. Kace, to, da Allah da ayoyinsa da Manzanninsa ne ku ke izgili? Kada ku bada hanzari, tabbas kun kafirta bayan imaninku. Idan mun yafe wa wata qungiya daga cikinku, to, zamu azabta wata qungiya domin sun kasance kangararru.

Kaicon wannan miskini ya na sukar mutanen da su ka qarar da rayuwarsu wajen taimakon addini. Ya za kayi suka ga wanda ya daxe da saukar da kayansa a cikin aljanna?

Malam Ibnu Asakir Ad Dimashqi yace, Lallai naman malamai akwai dafi a cikinsa, abin da Allah ya saba da shi kuwa na tonon asirran masu suka ga resu sananne ne, duk wanda ya saki bakinsa ya na suka ga malamai to, Allah zai jarabce shi da mutuwar zuciyarsa kafin mutuwar gangar jikinsa.

﴿فَلْيَحْذَرِ الَّذِينَ يُخَالِفُونَ عَنْ أَمْرِهِ أَنْ تُصِيبَهُمْ فِتْنَةٌ أَوْ يُصِيبَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ﴾ النور ٦٣

Ma'ana:
To, waxanda ke sava ma umurninsa su yi saunar kada fitina ta auka masu ko azaba mai raxaxi ta cim musu. Suratun Nur, Aya ta 63.

Qa'ida ta Bakwai: Adalci shi ne, auna yawan sawabar mutum tare da yawan kurakuransa.[21]

Wannan qa'ida ce ta zamantakewa a tsakanin mutane. Mutum duk xan tara ne, amma wani ladarsa ta rinjayi zunubinsa kamar yadda kyautatawarsa ta rinjayi kurakuransa. Wani kuma savanin haka ne zunubinsa ya fi ladarsa, varnarsa kuma ta fi gyaransa. Ba adalci ba ne muyi watsi da mutum don kawai ya yi wasu kurakurai sai mu turbuxe alherinsa.

Malam Sa'id binul Musayyib, xaya daga cikin fitattun malaman tabi'una yace, Ba wani malami ko basarake ko attajiri face ya na da lum'ah. Amma duk wanda alherinsa ya yawaita har ya rufe sharrinsa to, shi ne abin yabo. Wanda ko duk sharrinsa ya yi yawan da ya rufe alherinsa to, shi ne wanda ya kamata ayi suka akansa.[22]

---

20 Duba cikakken labarin a Tafsirin Ibnu Jarir Al Xabari (10/119).

21 Wannan qa'idar Ibnu Rajab ya faxe ta. Duba: *Qawa'id fit ta'amuli ma'al Ulama,* Shafi na 133.

22 *Jami'u Bayanil Ilmi Wa Fadlihi* (2/48).

## Taqaitaccen bayani akan matsayin gidan annabta

Akwai ababe da dama da ke nuna son Manzon Allah (SAW) waxanda suka haxa da darajanta iyalansa, da sonsu da jivintarsu da taimakonsu da kariyarsu, tare kuma da faxin matsayinsu da kyawawan ayyukansu, sannan da koyi da su.

An karvo hadisi daga Zaid binu Arqam (RA) yace, Manzon Allah (SAW) yace, "Ina tunayar daku Allah a game da iyalaina, Ina tunayar daku Allah a game da iyalaina, Ina tunayar daku Allah a game da iyalaina".[23]

Daga Abdullahi xan Abbas (RA) yace, Manzon Allah (SAW) yace, "Ku so iyalaina saboda sona".[24]

An karvo daga Abdullahi xan Umar (RA) yace, Abubakar Siddiq (RA) yace, ku kiyaye Manzon Allah (SAW) a iyalan gidansa.[25]

Don haka ne ya sa Sahabbai da Tabi'ai da sauran shugabannin musulmi magabata su ka kasance masu tsananin girmamawa da qauna ga iyalansa. Kamar yadda ya zo a cikin Sahihul Bukhari cewa, Abubakar Siddiq (RA) yace, Na rantse da wanda raina ya ke a hannunsa na fi son in sadar da zumuncin Manzon Allah (SAW) akan nawa.[26]

A lokacin da Abdullahi binul Hassan jikan Ali bin Abi Xalib ya je neman wata buqata a wurin sarki Umar bin Abdil Aziz, daga cikin sarakuna Banu Umayyah, sai sarkin yace masa, Daga yau ina fatar idan kana da wata buqata a wurina kar kazo da kanka, a maimakon haka ina son ka aiko xan saqo ko ka rubuto min wasiqa, domin ina jin kunyar Allah ya ganka a qofar gidana kana jira na.[27]

Shehun Malami Abul Walid Al Baji yace, Lokacin da sarki Al Mansur ya nemi Imam Malik ya xauki fansa akan gwamna Ja'afar binu

---

[23] Muslim ya fito da shi, Hadisi na 4425, a Fada'il Ali, Ahmad ma ya ruwaito shi, Hadisi na 18464 a farkon Musnadin Kufawa daga Zaid binu Arqam, kuma Darimi ya fitar da shi, Hadisi na 3182, a Fada'il Al Qur'an.

[24] Tirmidhi ya ruwaito shi, Hadisi na 3722, a darajojin Ahlu Baitin Nabiyyi. Tirmidhi xin kuma yace, ya na da kyau, amma yana da xan rauni.

[25] Bukhari ya ruwaito shi, a Babin darajojin dangin MAnzon Allah (SAW) daga Kitabu Fada'il As Sahabah, Hadisi na 3439.

[26] Bukhari ya ruwaito shi a Babin darajojin dangin Manzon Allah (SAW) daga Kitabu Fada'il As Sahabah, Hadisi na 3435. Kuma Muslim ya ruwaito shi, Hadisi na 3304, Babin faxar Annabi (SAW) cewa, ba a gadonmu. Kuma Ahmad ya fitar da shi, Hadisi na 52, a Musnadin Abubakar As Siddiq.

[27] *Dam'atu Ala Hubbin Nabiyy,* littafin da aka buga a jerin Kitabul Muntada Al Islami, *Huququn Nabiyyi (SAW) bainal Ijlali wal Ikhlal,* Shafi na 50.

Sulaiman wanda ya sa aka yi masa bulala bisa ga zalunci, sai Malik yace, "Allah ya kiyaye ni. Ai ba wata bulalar da aka xaga a kaina face na faxa a cikin raina cewa, na yafe masa saboda dangantakarsa da Manzon Allah (SAW).[28]

Shi ma Imamu Ahlis Sunnah, Ahmad binu Hambali lokacin da ya gamu da tasa jarrabawar, aka yi masa duka a zamanin sarki Al Wasiq, sannan daga baya Allah ya xaukaka al'amarinsa (Shi Ahmad), Sai Al Wasiq ya roqe shi ya yafe masa, sai yace, Daman can ni na yafe maka tun da farko saboda matsayin kakanka (SAW).[29]

Ga wani waqe mai armashi da Di'ibil Al Khuza'i ya yi game da son dangin Mustafa (SAW). A cikinta ya nuna tsananin qaunar da ya ke yi ga *Alhulbaiti* waxanda yace, ya fi sonsu da nasa dangin, kuma ba ya shiri da kowa idan ba mai qaunarsu ba ko da kuwa ciki xaya su ka fito.[30]

Wannan shi ne halin musulmi a duk in da aka fito.Amma a yau kam mutane sun kasu kashi a game da *Ahlulbaiti* kashi uku;

**Kashi na farko**: Su ne waxanda su ke tauye haqqensu, ba su kuma qaunarsu balai girmama su kamar 'yan Ibbadiyyah da su ka kauce ma wasicin Manzon Allah (SAW) akan su. Waxannan ba su da wata alaqa da Ahlus Sunnah sam.

**Kashi na biyu:** Su ne waxanda su ka faifaye a wajen sonsu har su ka wuce makaxi da rawa, ya kasance sun mayar da su kamar su ma manzanni ne, ko wani lokaci ma su allantar da su. Sai su na ta bada labaran qarya akan su wai don su ja hankalin wawaye da marasa ilmi zuwa ga shirmensu.

Shugabannin *Ahlulbaiti* kuwa tuni su ka yi Allah waddai da irin wannan so na hauka kamar yadda Ali binul Hussaini Zainul Abidin ya ke cewa, Ya ku mutane! Ku rinqa yi mana so irin na musulunci. A yanzu irin son da ku ke mana ya zama abinkunya akanmu.[31]

**Kashi na Uku:** Su ne tsaka tsaki, waxanda su ka tabbatar cewa, su dai *Ahlulbaiti* bayin Allah ne waxanda su ke kamar sauran mutane ta fuskar wajabcin bin Shari'ah da sauran abin da ya shafi 'yan adam na yanayin halitta, amma kuma Allah ya ba su wata daraja wadda ta samo asali daga kusancinsu da Manzon Allah (SAW). Don haka su kace a basu haqqensu.

---

[28] *Al Islam bainal Ulama'i Wal Hukkam,* na Abdul Aziz Al Badri, Shafi na 159, daga *Al Madarik,* na Alqali Iyal, Shafi na 293.

[29] *Dam'atu Ala Hubbin Nabiyy,* littafin da aka buga a jerin Kitabul Muntada Al Islami, *Huququn Nabiyyi (SAW) bainal Ijlali wal Ikhlal,* Shafi na 50.

[30] Baitocin waqar Di'ibil Al Khuza'i guda bakwai da mai littafi ya kawo ya na da matuqar wuya a fassara su kai tsaye zuwa harshen hausa musamman in ba ga gwanayen harshen ba kuma wataqila mawaqa. Abin da na faxa dai shi ne ma'anarsu. Mai karatu ya karvi uzurina. Daga Mai Fassara. Duba cikakkiyar waqar a littafin da ya gabata, Shafi na 50.

[31] *Al Xabaqatul Kubra,* (5/165) da *Hilyatul auliya'* (3/161), da *Tahdhibul Kamal,* (5/138), da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/374), da *Al Irshad* na Mufid (2/141) da kuma *Kashful Gummah,* na Arbili (2/297).

Sanin haqqen *Ahlulbaiti* da ba su waxannan haqqoqin wajibi ne tabbatacce a Shari'ah.[32] Don haka, ya kai musulmi, ka nemi sanin waxannan haqqoqi ka tsayar da su ban da wuce iyaka. Ka sani duk wanda ya kauce ma hanyar tsakiya zai halaka.

Allah ya yi muna dace da bin hanya madaidaiciya da tsarin tafiya miqaqqe.

[32] Idan kana son qarin haske game da haqqoqan *Ahlulbaiti* na Shari'ah ka duba littafin *Alul Bait Wa Huququhum As Shar'iyyah,* na xan uwana Sheikh Saleh Ad Darwish.

# FASALI NA XAYA
# Wane ne Zainul Abidin?

## Sunansa da Haifuwarsa

Sunansa Ali binul Hussain bin Ali bin Abi Xalib Al Hashimi Al Qurashi wanda aka fi sani da Zainul Abidin. Ana kuma ce da shi Baban Hassan.

Jikan Manzon Allah (SAW) ne ta wajen 'yarsa Fatimah Az Zahra'u (RA). Wannan dangantaka kuwa ta isa wajen xaukaka da daraja.

Mahaifiyarsa ita ce Salamatu, wasu masana kuma sunce sunanta Gazalatu. Amma 'yar Farisa ce ko 'yar qasar sindi ce? Wannan shi ne abin da masana su ka qari junansu sani akansa. Abin da aka tabbatar dai shi ne Ummu walada[33] ce ga mahaifinsa.

Ibnu Khillikan ya karkata ga ra'ayin farko, cewa mahaifiyarsa bafarisa ce, har ma yace, ana yi ma sa laqabi da "Ibnul Khairataini", xan mafifita biyu domin an ruwaito cewa, Allah ya na da zavavvu biyu, zavavvunsa a larabawa su ne Quraishawa, a ajamawa kuwa su ne Farisawa. [34]

Zamakhshari kuma cewa yayyi, Yazdajrid, Sarkin qarshe na Farisa ya na da 'ya'ya mata da aka kama su a zamanin sarki Umar xan khaxxabi, ta farkon ita ce aka bai wa Abdullahi xan Umar ta haifa masa Salim, ta biyu aka bai wa Muhammad binu Abi bakr ta haifa ma sa Qasim, ta ukun kuwa aka bai wa Hussaini bin Ali sai ta haifa ma sa Zainul Abidin, su ukun (Salim da Qasim da Zainul Abidin) kakansu xaya ne ta wajen iyayensu mata.[35]

Har wayau game da lokacin da aka kama ta, masana sun yi savani, ko lokacin khalifa Umar ne ko Usman.[36] To, ko wanne ne dai ya nuna yadda shugabannin *Ahlulbaiti* su ka yarda da waxannan khalifofi, su ka amince da ingancin jihadinsu da ganimomin da su ka samo. Ba don haka ba da Ali da 'ya'yansa ba su karvi ganimar har su ka haifar da waxannan 'ya'ya ba.[37]

---

[33] Ummu walada ita ce kuyanga wadda aka ganimance ta a wurin jihadi da zaran ta haifu ta samu wani yanki na 'yanci wanda ke hana a sayar da ita. Shi ya sa ake kiranta Ummu walada.

[34] *Sifatus Safwah,* (2/54) da *Siyar A'lam An Nubala'* (4/386).

[35] *Wafayat Al A'yan Wa Anba' Abna' Az Zaman,* (2/127).

[36] Duba littafin: *Al Imam Zainul Abidin Qudwatus Salihin,* na Ayatullahi Muhammad As Shirazi, da *Al Imam As Sajjad qudwatun wa Uswah,* na Muhammad Taqi Al Madrasi.

[37] Shi ma Sayyiduna Ali ya ribanci kuyangarsa Al Hanafiyyah ne a yaqoqan ridda da Sayyiduna Abubakar ya yi. Ita ce kuma ta haifa ma sa Muhammad Al Asgar wanda aka fi sani da Ibnul Hanafiyyah.

Ya'qub binu Sufyan yace, an haifi Ali binul Hussain a shekara ta 33 B.H.[38]

Amma a cewar Dhahabi ana zaton an haife shi ne a shekarar 38 B.H.[39] Wannan ra'ayin kuwa ya fi qarfi domin tarihi ya tabbatar da cewa, a lokacin da aka yi waqi'ar karbala' ya na da shekaru 23 ne.[40] Ita kuma waqi'ar karbala' ta faru a shekara ta 61 B.H. ne ba savani.[41]

---

38 *Tahdhib Al Tahdhib* (4/185) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/361).

39 *Siyar A'lam An Nubala'* (4/386).Su ma dai littafan Shi'ah sun yi savani akai. Duba littafin Shirazi da na Madrasi misali.

40 *Sifatus Safwah,* (2/54) da *Siyar A'lam An Nubala',* (4/386) da *Ax Xabaqat Al Kubra,* (5/163).

41 *AL Biadayah Wan Nihayah,* (5/173) da *Sifatus Safwah,* (1/344).

# FASALI NA BIYU

## Jihadinsa Da Yadda Ya Kuvuta A Karbala'

A cikin tarihi ba za ka tava karanta labari mai muni da tashin hankali ba kamar na Karbala'. Labari ne da ke tsage zuciya ya tsima jiki ya sanya ido zubar da hawaye. Ba don kome ba sai don zuri'ar Manzon Allah (SAW) da su ka gamu da ajalinsu a wannan karafkiya. Hussaini da akasarin iyalansa sun rasa rayukansu a wannan rana. Allah ya xaukake su da samun shahada don ya xaukaka darajarsu da matsayinsu a aljanna. Kusan ana iya cewa, ba wanda ya kuvuta daga cikinsu sai xansa Zainul Abidin wanda mu ke ba da tarihinsa a cikin wannan littafi. Shi ma ya yi saura ne a dalilin rashin lafiyarsa.

Malam Ibnu Sa'ad yace, Ali binul Hussaini ya kasance tare da mahaifinsa ya na da shekaru 23, amma a lokacin da aka zo Karbala' shi ba ya da lafiya, ya na kwance akan shimfixarsa. Bayan ma da aka kashe mahaifinsa Hussaini sai da Shamr binu Dhil Jaushan yace a kashe shi, amma wani mutum yace, don me za a kashe shi tun da bai yaqi kowa ba? Da Umar binu Sa'ad yazo sai yace, kar a kashe mata kar kuma a kashe wannan maras lafiya.[42]

Allah Sarki! Haka dai zamu ga wannan bawan Allah ya fito da cikakken shirinsa na yin yaqi tare da mahaifinsa amma Allah cikin ikonsa da ya ke ya nufi wanzuwar zuri'ar Hussaini sai ya kawo sanadin rashin lafiya wanda ya zama dalilin rashin mutuwarsa. In ban da vangarensa kuwa babu in da Sayyiduna Hussaini ya bar wata zuri'a wadda ta haxa jini da Manzon Allah (SAW) ta gefensa.

Malam Asma'i yace, Hussaini bai bar wata zuri'a ba sai ta wajen Ali binul Hussaini, shi kuma Ali bai bar wata zuri'a ba sai ta wajen matarsa kuma 'yar baffansa Ummu Abdillahi bintul Hassan.[43]

---

[42] *Al Xabaqat Al Kubra,* (5/163).

[43] *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/374) da *Siyar a'lam An Nubala',* (4/390) amma fa Dhahabi yace, isnadin maganar ya yanke.

# FASALI NA UKU
## Yabon da Mutane su kayi ma sa

Mutane su ne shedun Allah a bayan qasa. Duk musulmin da ka ga jama'a su nai ma sa kyakkyawan ambato da yabawa akansa ka tabbata ya na da rabo a wurin Allah kuma Allah ya na sonsa. A game da wannan bawan Allah kuwa Zainul Abidin shi sha yabo ne a wurin malamai. Wannan ko ita ce bushara ta farko ga mummuni.

Imam Malik ya na cewa, duk a gidan su Zainul abidin babu irinsa.[44]

Malam Zuhri kuwa, wanda shi ne malamin Malik cewa yayyi, ban tava ganin baquraishen da ya kai tsentseni da daraja irinsa ba.[45]

Malam Zirru binu Hubaish yace, Na kasance a wurin Ibnu Abbas sai Ali binul Hussaini yazo, Ibnu abbas ya yi ma sa maraba ya na mai cewa, maraba da masoyi xan masoyi.[46]

A lokacin da Hisham binu Abdil malik ya yi aikin hajji a khalifancin babansa tare da xan uwansa Walid yaje ya yi xawafi sai ya nufaci *Hajarul Aswad* don ya sumbace shi amma abin bai yiwu ba sai da aka kafa masa wani dandamali wanda ya hau akansa sannan ya sumbaci dutsen saboda cinkoso. Bayan haka ne sai mutanen Sham, hedikwatar mulki ta wannan lokaci su ka kewaye shi su na yi masa fadanci. Ana haka ne sai ya hangi Ali binul Hussaini ya gabato. A lokacin da ya kusanci dutsen sai duk mutane su ka janye ma sa aka ba shi dama ya sumbace shi don girmamawa, ga shi kuwa ya fito a cikin wata siffa mai kwarjini da ban sha'awa. Nan take sai mutanen Sham su ka ce masa, wai wane ne wancan? Sai yace, ban san shi ba, don kar ya jawo hankalinsu zuwa ga reshi. Sai mawaqin nan Firazdaq yace, ai ni na san shi, ku bari in ba ku labarinsa. Anan ne ya yi waqen nan nasa mai ban shawa in da ya wasa Zainul Abidin har sai da yarima Hisham yaji kunya shi da yace ban san shi ba.[47]

Malam Waqidi yace, Zainul Abidin na daga mafi tsentsenin mutane, mafi ibadarsu, kuma mafi tsoron Allansu.[48]

Malam Dhahabi kuwa ga abin da yace, Zainul Abidin ya na da kwarjini mai ban mamaki, kuma na rantse shi mai cancanta ne ga reshi. Tabbas ya dace da sarauta domin girmansa da matsayinsa da ilminsa da kammalar hankalinsa.[49]

---

[44] *Siyar A'lam An Nubala',* (4/389).
[45] *Al Bidayah Wan Nihayah,* (5/109) da *Sifatus Safwah,* (2/57) da *Siyar A'lam An Nubala',* (4/387).
[46] *Al Xabaqat Al Kubra,* (5/164) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/370).
[47] *Al Bidayah Wan Nihayah,* (5/114) da *Sifatus Safwah,* (2l57) da *Siyar A'lam An Nubala'* (4/398).
[48] *Al Bidayah Wan Nihayah,* (5/110).
[49] *Siyar A'lam An Nubala',* (4/398).

A taqaice wannan shi ne matsayin malamai na kirki akan wannan bawan Allah wanda xaya ne daga shugabannin iyalan gidan annabta. Su na sonsa, su na darajanta shi, su na yawaita yabo akansa, uwa uba kuma su na goyon bayansa da koyi da shi. Wannan ita ce aqidarmu Ahlus Sunnah game da duk iyalan Manzon Allah (SAW) wadda mu ke fatar Allah ya rayar da mu akanta, ya karvi rayukanmu akanta.

# FASALI NA HUXU
## Yawan Ibadarsa da qanqan da kansa ga Ubangiji

Dukkanmu mu na son kasancewa cikin xa'ar Allah, mu na sha'awar mu yawaita bautarsa da nau'oi na bauta da ya ke son a bautata ma sa da su. Amma nan take mun samu cikas da kasala saboda tasirin kwaxayinmu da bin son rayukanmu. Don haka ne mu ke da buqatar hanyoyin da za su taimaka mana wajen dagewa akan xa'a da bautar Allah maxaukakin Sarki. Daga cikin hanyoyin da za mu cimma wannan kuwa har da karanta tarihin magabata daga malaman farko waxanda rayuwarsu ta kasance tutur a cikin ibada kamar Zainul Abidin binul Hussain bin Ali. Ga kaxan daga cikin ababen koyi a rayuwarsa;

### Sallarsa da yawan addu'arsa

Imam Malik yace, Na samu labarin cewa, Zainul Abidin ya na sallah raka'a dubu a tsakanin kowane dare da wuni har Allah ya karvi ransa.[50] Yace, a dalilin yawan ibadarsa ne ma ake ma sa wannan suna Zainul Abidin, qawar masu bauta.[51]

Ja'afar binu Muhammad ya karvo daga babansa cewa, Ali binul Hussaini ya kasance ba ya barin qiyamul laili a tafiya ya ke ko a zaman gida.[52]

Shi ma Umar bin Ali abin da yace shi ne, Ali binul Hussaini ya kasance idan ya samu fargaba akan wani abu ya kan yawaita du'ai.[53]

Malam Xawus shi kuma cewa yayyi, Na ga Ali binul Hussaini ya na sujada a cikin *Hijr*, sai nace, wannan wani bawan Allah ne daga cikin iyalan tsarkakakken gida don haka bari inji abin da ya ke faxi. Sai na kusance shi naji ya na cewa, Ya Allah! Ga xan bawanka nan a bakin qofa, Ya Allah almajirinka ne a bakin qofa, Ya Allah talakanka ne a bakin qofa, Ya Allah! Miskininka ne a bakin qofa. Tun daga lokacin ni kuma na rinqa faxin irin hakan idan na shiga wani hali na qunci sai Allah ya kuranye min.[54]

Ko ka lura da yadda *Ahlulbaiti* su ke qanqan da kansu ga maxaukakin sarki? Su ba Allah ne ba, ba su iya amfanar da wani ko su cutar da shi. Su ma ta kansu su ke yi. Koma ga Allah ka huta da yaye yaye.

---

[50] *Sifatus Safwah,* (2/58) da *Siyar A'lam An Nubala'* (4/392) da *Tahdhib Al Kamal,* (5/239).
[51] *Tadhkiratul Huffazh,* (1/75).
[52] *Sifatus Safwah,* (2/55).
[53] *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/382)
[54] Littafin da ya gabata, (41/380).

## Yadda ya ke tsoron Allah da dogaro ga reshi

Duk wanda ya fahimci qasqantar duniya, ya gane girman alqiyama ba zai mayar da hankalinsa ga duniyar ba. Idan mutum ya daxa zurfafawa a wannan tunani ko abokin zama ba shi buqata. Wane irin daxi mutum zai ji idan ya tuna qabari ne makomarsa, kuma mala'ikan mutuwa na jiransa? Idan mutum ya na tuna ni'imar aljanna da azabar wuta wane daxin duniya ya ke buqata? Irin wannan shi ne tunanin Zainul Abidin a game da duniya. Duk abin da ke cikinta abin lura ne a gurinsa, ko wane shiru ko motsi wa'azi ne a ga reshi.

Abu Nuh Al Ansari ya faxi cewa, an yi gobara a wani gida da Ali binul Hussaini ya ke a cikinsa ya na sallah, aka yi dai dai kuwa ya na sujada, sai su ka rinqa cewa, Ya kai jikan Manzon Allah hattara da wuta! Amma bai xaga kansa ba har in da aka kashe wutar. Daga baya sai aka tambaye shi, yace, wutar da fi ta ce ta xauke hankalinsa, ya na nufin wutar jahannama. Allah ya kiyaye mu.[55]

Abdullahi binu Ja'afar Al Qurashi yace, idan Ali binul Hussaini ya yi alwalla fuskarsa ta kan canza, in aka tambaye shi sai ya kan ce, kun san ko a gaban waye zan tsaya?[56]

A ruwayar Sufyan binu Uyainah Ali binul Hussaini ya yi aikin hajji sai da ya yi harama ya hau dabbarsa sai yanayinsa ya canza, jikinsa ya rinqa vari ya na makarkata har ya kasa yin *Labbaika*. Anan ne mutane su ka tambaye shi me ya same ka? Sai yace, ina tsoron ince "Labbaika", na karva kiranka ya Allah, ace min "La Labbaika" ba a karvi kiranka ba. Sai aka ce masa, to, ai dole ne kace hakanan. A yayin da ya faxi hakan sai suma ya kama shi har ya faxo daga kan taguwarsa. Daga nan aka rinqa ganinsa a cikin wani yanayi har in da ya qare hajjinsa.[57]

## Karimcinsa da yawan sadaqarsa

Abu Hamzah As Sumali ya bada labarin cewa, Ali binul Hussaini ya kan xauki gurasa akansa ya zagaya ya na raba ta a gidajen matalauta cikin duhun dare. Ya kance, ina yin haka ne domin sadaka a cikin duhun dare ta na bice fushin ubangiji.[58]

Xansa Abu Ja'afar ya faxi cewa, sau biyu baban nasa ya na raba dukiyarsa biyu ya yi sadaka da kashi xaya.[59]

---

[55] *Sifatus Safwah,* (2/54) da *Siyar A'lam An Nubala',* (4'391) da *Tahdhibul Kamal,* (5/238).

[56] *Hilyatul Auliya',* (3/157) da *Siyar A'lam An Nubala',* (4'392) da *Ax Xabaqat Al Kubra,* (5/167) da *Tarikh Madinati Dimashq, (41/378).*

[57] *Tahdhibut Tahdhib,* (4/185).

[58] *Sifatus Safwah,* (2/56) da *Siyar A'lam An Nubala',* (4'393) da *Hilyatul Auliya',* (3/160) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/383).

[59] *Siyar A'lam An Nubala',* (4'393) da *Ax Xabaqatul Kubrah,* (5/196) da *Hilyatul Auliya',* (3/165) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/388).

Kuma idan zai bai wa miskini sadaka sai ya sumbace shi, ya nuna masa qauna sannan ya ba shi kamar yadda Abul Minhal Ax Xa'i ya ruwaito.[60]

An karvo daga Ja'afar binu Muhammad daga babansa cewa, Ali binul Hussaini ya kasance idan almajiri yazo masa ya kan yi maraba da shi ya na cewa, na yi murnar zuwan wanda zai xauki guzurina zuwa lahira.[61]

Wannan shi ne kai matuqa ga karimci. Mutum ya na sadaka kuma ya na ganin wanda zai karvi sadakar ya taimake shi? Irin waxannan mutane a yau sai dai mu karanta labarinsu a littafi, in ko har an gansu to, ba su wuce waxanda za a qirga ba. Muna roqon Allah ya yi muna dace.

Shaibah binu Nu'amah yace, mutane da yawa sun xauki Ali binul Hussaini marowaci ne, sai da ya rasu aka sami sama da gidaje xari waxanda ya ke xaukar nauyinsu.[62]

Malam Dhahabi yace, an xauki ya na rowa ne saboda ba ya yin sadaka a fili, a asirce yake yi sai a xauka shi marowaci ne tara kuxin yake yi.[63]

Muhammad binu Ishaq yace, Wasu mutane a Madina sun kasance su na rayuwa ba su san ta in da abincinsu yake zo mu su ba. A lokacin da Ali binul Hussaini ya cika sai su ka rasa abincin da ya ke zo mu su da dare. Masu yi ma sa wanka kuwa sai su ka ganshi da wasu alamomi a kafaxunsa da kuma akan bayansa saboda xaukar buhunan abinci da ya ke yi a cikin dare zuwa gidajen talakawa.[64]

Sufyan ya ba da labarin cewa, lokacin da Ali binul Hussaini ya nufi aikin hajji ko kuma Umrah, qanwarsa Sukainah bintul Hussaini ta aika ma sa da wata jaka mai xauke da kuxi kusan Dirhami 1000. A lokacin da ya kai wajen da ake kira *Harrah* sai ya yi umurni duk aka raba kuxin a tsakanin talakawa.[65]

Amru binu Dinar shi kuma ya ruwaito cewa, Ali binul Hussaini ya kai ziyara wurin Muhammad binu Usamah a lokacin rashin lafiyarsa, sai Muhammad ya rinqa kuka. Ali ya tambaye shi, me ka ke ma kuka? Sai yace, bashi ake bi na. Yace, har nawa ne hala? Yace, sama da Dinari 10,000 ne. Sai yace, to, ni zan biya.[66]

---

60 *Al Bidayah Wan Nihayah,* (5/120).

61 *Sifats Safwah,* (2/55).

62 *Sifatus SAfwah,* (2/55) da *Ax Xabaqatul Kubra,* (5/172) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/384).

63 *Siyar A'lam An Nubala',* (4'394).

64 *Siyar A'lam An Nubala',* (4'393) da *Hilyatul Auliya',* (3/160) da *Sifatus Safwah,* (2/56).

65 *Sifatus Safwah,* (2/56).

66 *Sifatus Safwah,* (2/58) da *Siyar A'lam An Nubala',* (4'394) da *Tahdhibul Kamal,* (5/239).

# FASALI NA BIYAR
## Tarin Ilminsa

Abdur Rahman binu Adrak yace, Ali binul Hussaini ya kasance ya kan shiga masallaci sai ya keta sahu don yaje wurin karatun Zaid binu Aslam. Sai Nafi'u binu Jubair yace masa, Allah ya taimake ka! Me ya sa kake ratsa jama'a don kaje wurin wannan bawa kayi karatu ga shi kuwa kai babban mutum ne a cikin mutane? Ali binul Hussaini sai yace, ai shi ilmi duk in da ya ke nemansa ake kuma can ake samunsa.[67]

Malam Zuhri yace, Na faxa Ali binul Hussaini wani hadisi, a lokacin da na qare faxa masa sai yace, ma sha Allahu! Ka kyautata, haka ne mu ma aka bamu labarinsa. Sai nace, to, ai ba wani abu ba ne face na faxa maka hadisin da ka fi ni saninsa. Sai yace, af! Ai duk karatun da ba a sani ba ba ilmi ba ne. Ilmi shi ne karatun da aka sani, harsunan malamai su ka yi ta bita akansa.[68]

To, ina masu ganin sun kevanta da wani sani koma bayan jama'a?

Ina 'ya'yan malam masu qaryar sani su na cika mutane da surrutu da labaran qarya don ace su ma malamai ne?

Ina masu qishirwar wa'azi waxanda duk in da suka zauna sai sun fesa qarya akan Manzon Allah (SAW) wai su suna kawo hadissansa? Sai su na tsinto ababen tausayi da ban mamaki daga cikin hadissan qarya don su burge mutane!

Duk waxannan sai su ji tsoron Allah. Ga maganar Zainul Abidin nan don su gane me nene ilmi? Ilmi shi ne karatun da aka sani, harsunan malamai su ka yi ta bita akansa.

Zainul Abidin dai masanin hadisi ne. Ya karanci hadisi a wurin malamansa daga cikin sahabbai kamar mahaifinsa Al Hussaini da baffansa kuma surukinsa Al Hassan, da iyayen mummunai Nana Safiyyah, Nana A'ishah, da Nana Ummu Salmah. Haka ma ya yi karatu wurin Abu Hurairah da Abu Rafi' dukkansu daga cikin almajiran Manzon Allah (SAW).[69]

Ko kana ganin malaman nasa ba na kirki ne ba? Sake nazari dai ka gani.

# FASALI NA SHIDA
## Kulawarsa da tsarkake zuciya

---

[67] *Siyar A'lam An Nubala',* (4'388) da *Hilyatul Auliya',* (3/162) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/369) da *Sharh Ihqaq Al Haqq,* na Sayyid Al Mura'shali, (28/453).
[68] *Tahdhibul Kamal,* (5/238) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/376).
[69] *Siyar A'lam An Nubala',* (4'387).

Lafiyar zuciya ita ce lafiyar sauran jiki kamar yadda cutarta ita ce rashin lafiyar jikin shi kansa. Don haka ne ma maxaukakin sarki ya keve ta ambato a tsakanin sauran gavvai in da ya ke cewa,

﴿ يَوْمَ لَا يَنْفَعُ مَالٌ وَلَا بَنُونَ (٨٨) إِلَّا مَنْ أَتَى اللَّهَ بِقَلْبٍ سَلِيمٍ (٨٩)﴾ الشعراء: ٨٨–٨٩

**Ma'ana:**
Ranar da dukiya ba ta amfani, haka ma 'ya'ya (Ba su amfani). Sai dai wanda yazo da zuciya lafiyayya.

Lafiyayyar zuciya ita ce wadda ba son bidi'a ko savon Allah a cikinta. Ita ce wadda ba da cuta ko aibi a tare da ita kamar qyashi ko hassada ko taurin kai ko makamantansu. Don haka ne magabata su ka yawaita mayar da hankulansu ga ayyukan zukata domin su kyautata alaqarsu da mahalicci mai girmama da xaukaka. Ga wasu 'yan misalai daga rayuwar wannan bawan Allah;

**Tawali'unsa:**

An karvo daga Abdullahi binu Abi Sulaiman yace, Ali binul Hussaini ya kasance idan ya na tafiya ba ya taqama, hannayensa ma ba su wuce cinyarsa.[70]

Ja'afar binu Muhammad shi kuma yace, Ali binul Hussaini ya kasance idan ya na tafiya a kan alfadarinsa cikin qananan hanyoyin Madina bai ce ma mutane gafara dai, ya na ganin hanya ta kowa ce, dole ne abar kowa ya tafi yadda ya ke so.[71]

Xansa Ja'afar binu Muhammad ya gamu da wasu baqi sai su ka rinqa wasa shi su na yaba masa, sai yace, ai idan mun kasance cikin na kirki ma ya ishe mu.[72]

Wannan ita ce hanya mafi kyau wajen karya girman kai, mutum ya nisantar da kansa daga qaunar a yabe shi, kamar yadda magabatan farko su keyi su na qyamar a yaba ma su don gudun Allah ya yi fushi da su ko ya qyamace su idan ba hakanan su ke ba a wurinsa. Allah Ta'ala kuwa ya sifaita masu rabo a lahira da cewa,

﴿تِلْكَ الدَّارُ الْآخِرَةُ نَجْعَلُهَا لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ عُلُوًّا فِي الْأَرْضِ وَلَا فَسَادًا وَالْعَاقِبَةُ لِلْمُتَّقِينَ (٨٣)﴾ القصص: ٨٣

**Ma'ana:**
Waccan ita ce gidan lahira, muna sanya ta ga waxanda ba su son xaukaka a cikin qasa, hakanan (Basu son) varna. Qarshen qwarai ya na ga masu tsoron Allah.

---

[70] *Sifatus Safwah,* (2/54).

[71] *Siyar A'lam An Nubala',* (4'398) da *Musnad Ar Rida,* na dawud Al Gazhi, Shafi na 160, da *Sharh Ihqaq Al Haqq,*na Sayyid Al Mura'shali, (28/105)

[72] *Siyar A'lam An Nubala',* (4'388) da *Hilyatul Auliya',* (3l162) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/369) da *Al Irshad* na Mufid (2/143) da *Biahrul Anwar,* (46/74).

Ka'ab binu Malik (RA) yace, Manzon Allah (SAW) yace, Kerkeci biyu idan aka sake su a garken awaki ba za suyi varnar da kwaxayin mutum akan dukiya da girman duniya ke yi masa a addininsa ba.

## Haqurinsa:

Wani mutum ya zagi Zainul Abidin sai ya fita batunsa kamar ma bai ji shi ba. Sai yace, da kai ni ke fa! Zainu yace masa, ni kuma ba ka dame ni ba.[73]

Abdul Gaffar binul Qasim yace, Ali binul Hussaini ya kasance ya na wajen masallaci sai wani mutum ya zage shi. Nan take bayi da yara su kayi ciri a cikinsa. Sai Ali yace masu, ku rabu da shi mana! Sannan ya fuskance shi ya na cewa, abin da ka faxi kaxan ne ka sani. Kana da wata buqata ne a biya ma ka? Wannan mutum sai ya rasa abin da zai ce ma sa saboda jin kunya. Sai Ali ya xauko wata riga ya ba shi, sannan yace a ba shi Dirhami 1000. Daga ranar duk su ka haxu sai yace da shi, na shaida kai jikan Manzon Allah ne (SAW).[74]

## Afuwa da Rangwame:

Malam Ibnu Abid Dunya ya ruwaito cewa, wani saurayi da ya ke aiki a gidan Ali binul Hussaini yaje zai yanka nama sai wuqa ta faxi akan xan mai gidan. Kafin kace kwabo kuwa yaron ya mutu. Hankalinsa ya tashi ainun, amma shi dai Zainul Abidin ba abin da yace ma sa face, na sani ba da gangan ba ne. Sannan yaje zuwa janaizar xansa.[75]

Abu ya'qub Al Madani yace, an samu rashin jituwa a tsakanin Hassan binul Hassan da xan baffansa Ali binul Hussaini, sai Hassan yazo da jama'arsa a cikin masallaci su na gaya ma sa munanan maganganu, shi kuma Ali bai ce komai ba. Sai da dare ya yi sai Ali ya same har gida ya sallama ma sa, da ya fito sai yace da shi, ya xan uwana! Duk abin da ka faxi a game da ni idan gaskiya ne ina roqon Allah ya yafe min. Idan kuma qarya ne ina roqon Allah ya yafe ma ka. Sannan sai ya juya ya tafiyarsa. Wannan abin kuwa sai ya ba xan uwansa mamaki, ya bi shi ya rungume shi ya na ba shi haquri har ya na kuka ya na cewa, wallahi ba zan qara yin haka ba. Shi kuma Ali yace, to, in haka ne ai ni tuni ma na yafe ma ka.[76]

Abdur Razzaq yace, wata kuyanga daga cikin bayin Ali Zainul Abidin ta yi tuntuve a lokacin da ta kawo ma sa ruwan alwalla, sai shantali ya kife a fuskarsa har ya yi ma sa rauni. Da ya xaga kansa sai tace ma sa, ka yi haquri, ka san Allah yace,

---

[73] *Tahdhibul Kamal,* (5/240).

[74] Duba littafin da ya gabata.

[75] *Sifatus Safwah,* (2/75) da *Al Bidayah Wan Nihayah* (5/113).

[76] *Sifatus Safwah,* (2/55).

﴿وَالْكَاظِمِينَ الْغَيْظَ..﴾

Ma'ana;
"Da waxanda su ke haxiye fushi (Su ne masu tsoron Allah)".
Sai yace ma ta, na haxiye.
Sai ta ci gaba da karanta ma sa,

﴿وَالْعَافِينَ عَنِ النَّاسِ..﴾

Ma'ana:
"Da masu yafe wa mutane",
Yace ai na yafe ma ki.
Sai ta qarasa ayar

﴿وَاللهُ يُحِبُّ الْمُحْسِنِينَ﴾ سورة آل عمران: ١٣٤

Ma'ana:
"Allah ya na son masu kyautatawa".
Sai yace, ki tafiyarki na xiyauta ki.[77]

Wa zai iya wannan in ba babban mutum ba? Haxa yafewa da kyautatawa shi ne kamala ta masu tsoron Allah. Shugabannin *Ahlulbaiti* kuwa sun cancanta su ba mu misali irin wannan da Zainul Abidin ya ba mu. Ko wanensu zuciyarsa fara ce swal, ba ya qyashi ko jin haushin kowa, ba ya kuma riqo idan aka munana ma sa. Kowannensu kamar yadda wani mawaqi yace ne,
Na xora wa kaina yin afuwa ga duk mai laifi
Kome girman kurakuransa.
Domin mutane iri uku ne,
Wanda ya fi ni ko wanda na fi shi ko wanda mu ke kunnen doki.
Wanda ya fi ni na san girmansa,
Zan bi gaskiya in ba shi haqqin girmansa.
Wanda na fi shi ba na raina kaina wajen faxa da shi,
Wanda kuwa mu ke kunnen doki,
Ni kan riga shi wajen yin afuwa domin ita ce halin girma.[78]

[77] *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/387).
[78] Wanda ya yi wannan waqar a larabce shi ne, Mahmud Al Warraq, wanda ya rasu a shekara ta 225 B.H. Ka duba littafin *Al Mustaxraf fi Kulli Fannin Mustazraf*, shafi na 205.

Yarda da qaddarar Allah:

Xabarani ya ruwaito cewa, watarana Zainul Abidin ya na zaune tare da wasu mutane sai ya ji ana kiransa daga cikin gidansa. Nan take ya tashi ya shiga a ciki. Da ya dawo bai ce ma kowa qala ba, sai daga baya aka gane ashe rasuwa aka yi a cikin gidan nasa. Mutane su kayi ta mamakin haqurinsa har sai da aka yi ma sa magana akan haka, sai yace, mu a gidanmu an koya ma na idan abin murna ya samu mu bi Allah, idan na damuwa ya samu kuma mu gode ma sa.[79]

Wannan shi ne abin koyi ga dukkan musulmi. Domin qaddarori na Allah akwai alheri mai yawa a tattare da su, idan ka yi haquri za ka same su. Raki da kuka da dukan jiki ba su canza hukuncin Allah. Don haka, xan uwa haqurtar da kanka, ka kore damuwa, ka daina raki. Ka nemi taimakon Allah akan haquri idan musiba tazo ma ka. Ka sani mahaqurci shi ne mawadaci.

Allah Ta'ala yace,

﴿إِنَّمَا يُوَفَّى الصَّابِرُونَ أَجْرَهُمْ بِغَيْرِ حِسَابٍ﴾ سورة الزمر: ١٠

Ma'ana:

Lalle ne ana ba masu haquri ne kawai ladarsu ba tare da lisafawa ba.

Tsentseni:

Malam Juwairiyah binu Asma'u yace, Ali binul Hussaini bai tava cin ko taro albarkacin zumuntarsa da Manzon Allah (SAW) ba.[80]

Haka ne. Wannan ita ce cikakkiyar kariya ga zumuntar Manzon Allah (SAW). Ba daidai ba ne a xauke ta a matsayin hanyar neman duniya. Wannan zumunci daraja ce da Allah ya ba su, ya xora ma su kare haqqenta ta fuskar tsayar da Shari'ah da kyautata ma al'umma da kariyar addini.

---

[79] *Hilyatul Auliya'* (3/162) da *Tahdhibul Kamal,* (5/239) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/386).

[80] Yana nufin kuxin garawa. Duba *Siyar A'lam An Nubala',* (4/391) da *Tahdhibul Kamal,* (5/238) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/377).

# FASALI NA BAKWAI
## Wannan Ita ce Aqidarsu

### Na xaya: Su na sallah bayan ko wane musulmi

An karvo daga Muhammad binul Furat Al Tamimi yace, na zauna kusa da Ali binul Hussaini a masallacin juma'a sai wasu mutane su ka rinqa magana akan limanci. Sai ya tambaye ni me suke  cewa? Sai nace masa, 'yan Shi'arku ne, wai su na cewa, ba ya halalta ayi sallah a bayan Banu Umayyah. Sai yace, wannan wallahi bidi'a ce. Duk wanda ya karanta Alqur'ani, ya fuskanci alqibla kuyi sallah bayansa, idan na kirki ne don kansa, in ba haka ba kuma kansa.[81]

Daga Abu Ja'afar yace, mu na sallah a bayansu – Banu Umayyah – ba don taqiyyah ba. Kuma na sheda cewa, Ali binul Hussaini ya na sallah bayansu ba don taqiyyah ba.[82]

Haka ne ya kamata masoyan *Ahlulbaiti* da masu neman haxin kai su fahimci musulunci fahimta ingattacciya. Domin a yau wasu sun daina sallar jam'i sun daina ta jum'ah, sun haramta wa kansu lada mai tarin yawa da alheri mai girma wai don babu shugaba ma'asumi wanda zai jagorance su.

Ya kai xan uwa musulmi! Yi nazarin waxannan hadissai guda biyu:

1. Manzon Allah (SAW) yace. "... Su na yi muku sallah, idan sun yi daidai za ku samu lada tare. Idan kuwa sun kauce su ne za su cutu, ku kuma ladarku ta na nan".[83]
2. Manzon Allah (SAW) yace, "Sallolin farillah wajibai ne akan ko wane musulmi ya yisu a bayan limami musulmi, na kirki ne ko ba na kirki ba ko da ya na aikata manyan zunubbai.[84]

### Na biyu: Sun yarda da Sahabbai

An karvo daga Abu Hazim yace, wani mutum yazo wurin Ali binul Hussaini sai yace, me nene matsayin Abubakar da Umar a wurin Manzon Allah (SAW)? Ali binul Hussaini yace masa, irin matsayinsu a yanzu. Ya nuna qaburburansu. Ya na nufin yadda su ke a kwance yanzu kusa da juna haka kusancinsu ya ke a lokacin rayuwarsu, haka kuma ya ke a aljanna.[85]

---

[81] *Tahdhibul Kamal,* (5/240) da *Jiahdul Imam As Sajjad,* na Muhammad Rida Al Jalali, Shafi na 109.

[82] *Ax Xabaqatul Kubra,* (5/163).

[83] Bukhari ya fitar da shi a Kitabul Adhan, Babin idan Liman bai cika Sallah ba amma Mamu ya cika.

[84] Abu Dawud ya ruwaito shi a Kitabus Salati, Babin limancin na gari da mugu.

[85] *Siyar A'lam An Nubala',* (4/395) da *Tahdhibut Tahdhib,* (4/185) da *Tahdhibut Tahdhib,* (5/239).

Daga Ja'afar binu Muhammad daga babansa yace, wani mutum yazo wurin babana, yana nufin Zainul Abidin Ali binul Hussaini, yace, Ba ni labarin Abubakar. Sai yace, Siddiq ka ke nufi? Sai mutumin yace masa, kai ma ka na kiransa haka? Sai yace, kai ar! Ba ka waxanda su kayi masa wannan suna ba? Waxanda su kayi masa wannan suna ai sun fi ni. Manzon Allah ne (SAW) da Muhajirai da Ansarai. Wanda ko duk bai kira shi "Siddiq" mai cikakkiyar gaskatawa ba, to kada Allah ya gaskata maganarsa. Ni ina ba ka shawarar kaje ka so Abubakar da Umar, ka qaunace su, in hakan laifi ne na xauke maka.[86]

Muhammad binu Haxib yace, wasu mutane sunzo ma Ali binul Hussaini daga Iraqi, sai suka rinqa aukawa a cikin mutuncin Abubakar da Umar da Usman (R.A). To, a lokacin da suka qare kalamansu sai Imam yace da su: Ku ba ni labari su wane ne ku? Shin ku ne Muhajirai na farko da Allah Ya ce:

﴿لِلْفُقَرَاءِ الْمُهَاجِرِينَ الَّذِينَ أُخْرِجُوا مِنْ دِيارِهِمْ وَأَمْوَالِهِمْ يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِنَ اللهِ وَرِضْوَانًا وَيَنْصُرُونَ اللهَ وَرَسُولَهُ أُولَئِكَ هُمُ الصَّادِقُونَ (٨)﴾

Ma'ana:
(Ku yi mamaki) ga matalauta masu hijira waxanda aka fitar daga gidajensu da dukiyoyinsu, suna neman falala daga Allah da kuma yarda, kuma suna taimakon Allah da manzonSa! Waxannan su ne masu gaskiya.

Suratul Hashri, Aya ta 8.

Sai su ka ce, A`a. Ya ce: to, ku ne:

﴿وَالَّذِينَ تَبَوَّءُوا الدَّارَ وَالْإِيمَانَ مِنْ قَبْلِهِمْ يحُِبُّونَ مَنْ هَاجَرَ إِلَيْهِمْ وَلَا يجَِدُونَ فِي صُدُورِهِمْ حَاجَةً مِمَّا أُوتُوا وَيُؤْثِرُونَ عَلَى أَنْفُسِهِمْ وَلَوْ كَانَ بِهِمْ خَصَاصَةٌ وَمَنْ يُوقَ شُحَّ نَفْسِهِ فَأُولَئِكَ هُمُ الْمُفْلِحُونَ (٩)﴾

Ma'ana:
Da waxanda suka zaunar da gidajensu (ga musulunci) kuma (suka zavi) imani, a gabanin zuwansu, suna son wanda ya yi hijira zuwa gare su, kuma ba su tunanin wata buqata a cikin qirazansu daga abin da aka bai wa muhajirai, kuma suna fifita waxansu a kan kawunansu, kuma ko da suna da wata larura. Kuma wanda aka kiyaye shi daga rowar ransa to, waxannan su ne marabauta.

Suratul Hashri, Aya ta 9.

Sai su ka ce, A`a. Ya ce: To, ga shi ku kun sheda ba ku cikin waxannan biyun. Ni kuma na shaida ba ku cikin na ukkun su ne:

[86] *Siyar A'lam An Nubala',* (4/395) da *Tahdhibul Kamal,* (5/239) da *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/388) da *Jihadul Imam As Sajjad,* Shafi na 103.

﴿وَالَّذِينَ جَاءُوا مِنْ بَعْدِهِمْ يَقُولُونَ رَبَّنَا اغْفِرْ لَنَا وَلِإِخْوَانِنَا الَّذِينَ سَبَقُونَا بِالْإِيمَانِ وَلَا تَجْعَلْ فِي قُلُوبِنَا غِلًّا لِلَّذِينَ آمَنُوا رَبَّنَا إِنَّكَ رَءُوفٌ رَحِيمٌ (١٠)﴾

Ma'ana:
Kuma waxanda suka zo bayansu, suna cewa, "Ya Ubangijinmu! Ka yi gafara a gare mu, kuma ga 'yan uwanmu, waxanda suka riga mu yin imani, kada Ka sanya wani qulli a cikin zukatanmu ga waxanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu! Lalle Kai ne Mai tausayi, Mai jinqai. Suratul Hashri, Aya ta 10.

Sa`annan ya ce da su: Ku fita ku bani wuri. Allah Yayi mu ku kaza da kaza (ma`ana yayi addu`a maras kyau akansu).[87]

A wata ruwaya kuma cewa yayyi, Ku tashi ku ba ni wuri! Kada Allah ya kusanta gidajenku domin ku ku na lavawa ne ga musulunci don kuyi varna, amma ku ba musulmi ba ne.[88]

Akwai mamaki ga waxannan mutane da irin qarfin halinsu wajen sukar Sahabban Manzon Allah (SAW), da yadda ta qoqarin rusa musulunci.

Wa nene ya kawo ma na Alqur'ani?

Wa nene ya cirato mana rayuwar Manzon Allah (SAW) da ayyukansa?

Wa nene ya xauko musuluncin kacokan bayan ya yi jihadi wajen kariyarsa, ya kutsa birni da qauye ya na yaqi, don ya isar da shi zuwa ga remu?

Su wa nene Allah yace, ya yarda da su kuma sun yarda da shi?

Duk waxannan ba su ne Sahabban Manzon Allah (SAW) ba? Ba sune surukansa ba? Sun yi tarayya kuma da shi a wasu jikoki.[89]

Duk mai sukar su to, addinin ne yake suka. Wanda ya soke su ba sauran Alqur'ani a gurinsa don ba shi da hanyar saninsa.

Wanda ya tuhumce su da sun canza wani abu a cikin littafin Allah kuwa, to, littafin Allah xin ya qaryata shi.

Wanda yace sun canza bayan Manzon Allah (SAW) sun yi ridda bai yarda da abin da Allah yace ba kenan cewa, ya yarda da su. Domin kuwa ya za'a yi wanda Allah ya yarda da shi ya bar shi ya vace har ya kai ga ridda?

---

[87] *Sifatus Safwah,* (1/56) da *Hilyatul Auliya'* (3/161).

[88] *Al Bidayah Wan Nihayah,* (5/112) da *Tahdhibul Kamal,* (5/239) da *Al Fusul Al Muhimmah,* na Ibnus Sabbag (2/864) da *Kashful Gummah,* na Arbili, (2/291).

[89] Misali Ja'afar Al Sadiq, mahaifiyarsa ita ce, Ummu Farwa Bintul Qasim bin Muhammad bin Abibakar. Don haka, Sayyiduna Abubakar shi ne kakan Al Sadiq da Al Kazim da Al Hadi da Ar Rida da Al Jawad duk daga cikin *Ahlulbaiti.*

# FASALI NA TAKWAS

## Wafatinsa

An karvo daga Abu Ja'afar cewa, lokacin da mutuwa tazo ma mahaifinsa Ali binul Hussaini ya yi kuka. Sai nace masa baba me ya sa ka kuka alhalin kuwa ni ban tava ganin wanda ya bautata ma Allah kamarka ba?

Sai yace, Ya xana! Idan Alqiyama ta yi ba sauran mai iko. Kowa ya na a qarqashin ikon Allah har Annabawa da Mala'iku. Wanda Allah yaso sai ya kai shi aljanna, wanda yaso kuwa sai a yi wuta da shi.[90]

Ali binul Hussaini ya rasu a shekara ta 95 B.H. kamar yadda Malam Yahya binu Kasir yace.[91]

Amma wasu masana sunce, a shekara ta 94 B.H. ya rasu, ya na da shekaru 58 a duniya. Wasu masanan kuwa na da ra'ayin cewa, tun a shekarar 92 ko 93 B.H. ne Allah ya karvi ransa.[92]

Bayan yi masa sallah an kai shi a maqabartar baqi'ah in da aka yi jana'izarsa.

Anan ne za ka ga qarshe na gaskiya ga wannan rayuwa. Allah mabuwayi yace,

﴿إِنَّكَ مَيِّتٌ وَإِنَّهُمْ مَيِّتُونَ﴾ سورة الزمر: ٣٠

Ma'ana:
Lalle ne kai (Manzon Allah) mai mutuwa ne, Kuma lalle ne su ma masu mutuwa ne.

Suratuz Zumar, aya ta 30

﴿وَمَا جَعَلْنَا لِبَشَرٍ مِنْ قَبْلِكَ الْخُلْدَ أَفَإِنْ مِتَّ فَهُمُ الْخَالِدُونَ﴾ سورة الأنبياء : ٣٤

Ma'ana:
Ba mu sanya ma wani mutum tabbata ba a gabaninka. To, idan ka mutu su za su dawwama ne?

Suratul Anbiya' aya ta 34

Wannan ita ce rayuwar xan adam. Kome tsawon ranka watarana zaka mutu. Ko wane ne abokinka watarana zaka rabu da shi.

Kaji daxi yadda ka ke so, amma fa tabbas sai ka rabu da shi. Mutuwa kenan! Mai wargaza jin daxi, mai kore farin ciki. Wasu lokuttan mu tuna, a wani yanayin kuma sai mu shimga.

Ali binul Hussaini bai yi kuskure ba da yace a cikin wani waqensa;
Mu kan firgice idan mutuwa ta juyo
Mu na koma wasarmu idan mun ka mance

---

90 *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/379).
91 *Siyar A'lam An Nubala',* (4/400).
92 *Al Bidayah Wan Nihayah,* (5/119).

Misalin namu wanda ya hangi zaki
Idan ya ba da bai ko sai ya mance[93]

[93] *Tarikh Madinati Dimashq,* (41/410).

## Kammalawa

Ya xan uwa!

Ga mu dai tare da kai mun kammala wannan saqo, bayan mun yawata a cikin tarihin wannan bawan Allah wanda xaya ne daga fitattun 'yan gidan annabta, kuma wanda 'yan sha biyun shi'a ke gadara da jingina kansu zuwa ga reshi.

Daga abin da ya gabata dai ka na iya fahimtar wane ne Zainul Abidin bisa gaskiyar Allah babu za'ida. Mu na iya taqaita darussan wannan xan littafi kamar haka;

Darasi Na xaya

Tataccen tauhidi shi ne aqidar da *Ahlulbaiti* su ka rayu akansa. Ba su kiran kira kowa don neman biyan buqatunsu sai mahaliccinmu. Ba su kiran Annabi ko Mala'ika ko Waliyyi ko wani zavavve, domin sanin da su kayi cewa, wannan haqqen Allah ne shi kaxai. Ba mai amfanar kansa da kome a duniya sai da yardar Allah ballantan ya amfani wani. Wanda ko Allah ya nufi shi da samun cuta ba mai kuranye ta daga kunsa sai shi Allah mahalicci.

Ga abin da Allah yace ma mushrikai da su ka nemin agajin wani ba shi ba;

﴿إِنَّ الَّذِينَ تَدْعُونَ مِنْ دُونِ اللَّهِ عِبَادٌ أَمْثَالُكُمْ فَادْعُوهُمْ فَلْيَسْتَجِيبُوا لَكُمْ إِنْ كُنْتُمْ صَادِقِينَ﴾ سورة الأعراف: ١٩٤

Ma'ana:

Lalle ne duk waxanda ku ke kira koma bayan Allah su bayi ne irinku. To, sai ku kira su, su kuma su karva maku in har kun kasance masu gaskiya (a kiran da ku ke ma su). Suratul A'raf, aya ta 194

Darasi Na biyu;

Kyakkyawar alqar da ke tsakanin Sahabbai da *Ahlulbaiti*, iyalan gidan Manzon Allah (SAW). Wannan hujja ne akan soyayyar gakiya da qaunar da su ke ma junansu.

Sau tari ne *Ahlulbaiti* su ka kare martabar almajiran mai gidansu, su na yaba ma su, su na mayar da martani akan mai sukarsu, su na jaddada kira ga qaunarsu da jivintarsu. Wannan kuwa ba zai asali ba da kyakkyawan yabon da Allah ya yi ma su (Sahabban) a cikin tsarkakakken littafinsa, kamar in da ya ke cewa;

﴿لَقَدْ تَابَ اللهُ عَلَى النَّبِيِّ وَالمُهَاجِرِينَ وَالْأَنْصَارِ الَّذِينَ اتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ الْعُسْرَةِ مِنْ بَعْدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ فَرِيقٍ مِنْهُمْ ثُمَّ تَابَ عَلَيْهِمْ إِنَّهُ بِهِمْ رَءُوفٌ رَحِيمٌ﴾ سورة التوبة: ١١٧

Ma'ana:

**Darasi na Uku:**

Irin kyawawan xabi'un wannan bawan Allah kamar son jama'a da kyautata ma su, da haquri akan cutawarsu, da nisantar abin hannunsu duk su na daga cikin xabi'un annabta da ya gada daga iyaye da kakanninsa.

**Darasi na Huxu;**

Cikakken tsoron Allah shi ne wanda ya ya ke gadar da yin aiki da tsare ibada. Zainul Abidin kuwa ya dace da wannan suna nasa a wannan fage.

**Darasi na biyar;**

Qarya ne ace Ahlus Sunnah su na gaba da *Ahlulbaiti* a da ko a yanzu, domin kuwa babu wanda ya san haqqensu bisa ga adalci kamar Ahlus Sunnah. Mu tuna irin yabon da limaman Sunnah su ka yiwa wannan bawan Allah. Haka su ke da duk sauran ire irensa daga zuri'ar Annabi mai tsarki.

**Daga qarshe,** Ina 'yan uwana masu qaunar iyalan Manzo, masu jin daxin jingina kansu zuwa ga resu? A daina faxin maganar fatar baki wadda ba ta kai zucci. A koma ma rayuwar waxannan bayin Allah ayi koyi da su a maganganunsu da ayyukansu. Masoyi fa shi ne mai koyi da masoyinsa.

Wannan kiran na fara shi da kaina sannan da sauran 'yan uwana musulmi na ko wace xariqa da ko wace mazhaba. Muzo muyi aiki da kalamai da ayyukan *Ahlulbaiti* don mu haxa kanmu wuri xaya kamar yadda su ka kasance a tasu rayuwa, wataqila zamu samu haske da zai kai mu wurin Allah mu same shi a cikin yarda da mu ba cikin hushi ba.

Ya Allah! Ga yi gafar ga remu da 'yan uwanmu musulmi da su ka riga mu bada gaskiya, Kada ka sanya damuwa a cikin zukatanmu a game da waxanda su ka yi imani. Lalle ne ya Ubangijinmu Kai ne Mai tausyi, Mai jinqai.

Allah ya yi tsira akan annabinmu Muhammad da iyalansa da Sahabbansa baki xaya.[94]

[94] An gama wallafa wannan littafi da hantsin ranar Arafah a shekarar 1426 B.H Kuma ni ne bawa mabuqaci zuwa ga Allah, Abdu Aziz binu Ahmad bin Abdillaxif Al Umair. Mai fassara kuma ya kammala a yau daren assabar 20 ga Shawwal 1427 B.H. a Kaduna. Allah ya sa mu yi tarayyar lada a wannan aiki, ya sa mu samu ceton Manzonsa don qaunarmu ga iyalansa.

## Manazarta

*Al Bidayah Wan Nihayah,* na Ibnu Kathir Ad Dimashqi, Bugun Farko, Dar Ar Rayyan Lit Turath.
*Tarikh Madinati Dimashq,* na Hafizh Ibnu Assakir As Shafi'i, Dar Al Fikr.
*Tahdhib Al Kamal,* na Hafizh Ibnu Hajar Al Asqalani, Bugun Farko, Muassasatur Risalah.
*Tahdhib At Tahdhib,* na Hafizh Ibnu Hajar Al Asqalani, Bugun Farko, Dar Al Ma'rifah.
*Al Jami' As Sahih,* na Imam Abu Isa At Tirmidhi, Bugun Farko, DAr Ihya' At Turath.
*Hilyatul Auliya' Wa Xabaqatul Asfiya',* na Hafizh Abu Nu'aim Al Asfahani, Bugun Farko, Dar Al Kutub Al Ilmiyyah.
*Dam'atun Ala hubbin Nabiyy,* na Abdullahi binu Saleh Al Khudairi, An buga shi a jerin littafan Al Muntadal Islami, *Huququn Nabiyy bainal ijlali Wal Ikhlal,* Bugun Farko.
*Siyar A'lam An Nubala',* na Imam Shamsud Din Muhammad binu Ahmad Addhahabi, Bugu na Sha xaya, Muassasatur Risalah.
*Sahih Al Bukhari,* na Imam Muhammad binu Isma'il Al Bukhari, Dar Al Qalam, Beirut.
*Sahih Muslim,* na Imam Muslim binul Hajjaj, Dar Ihya' At Turath Al Arabi.
*Sifatus Safwah,* na Imam Ibnul Jauzi, Bugun Farko, Dar Al Fikr.
*Ax Xabaqat Al Kubra,* na Imam Ibnu Sa'ad Al Basri, Bugu na biyu, Dar Al Kutub Al Ilmiyyah.
*Musnad Al Imam Ahmad,* na Imam Ahmad binu Hambal, Dar Al MA'arif.
Littafan Shi'ah:
*Bihar Al Anwar,* bugun Al Wafa, Beirut, 1403H.
*Sharh Ihqaq Al Haqq,* na Al Mura'shali, Maktabatu Ayatillil Uzhmah Al Mura'shali, Qum, Iran, 1415H.
*Kashful Gummah,* na Arbili, Bugun Al Adwa', Beirut.